رئاسة الشؤون الدينية
بالمسجد الحرام والمسجد النبوي

# YADDA AKE UMARA

## Tare da zaɓaɓɓun addu'o'i

Guzurin manufatan Masallatai biyu masu alfarma

مطبوعات قاصد الحرمين الشريفين

برنامج قاصد الحرمين

رئاسة الشؤون الدينية
بالمسجد الحرام والمسجد النبوي

# YADDA AKE UMARA

## Tare da zaɓaɓɓun addu'o'i

### Guzurin manufatan Masallatai biyu masu alfarma

ⓗ رئاسة الشؤون الدينية بالمسجد الحرام والمسجد النبوي، ١٤٤٦هـ
رئاسة الشؤون الدينية بالمسجد الحرام والمسجد النبوي
صفة العمرة باللغة الهوساوية./رئاسة الشؤون الدينية بالمسجد الحرام والمسجد
النبوي - ط١. .- مكة المكرمة، ١٤٤٦هـ
٤٣ص، ١٤×٢١سم
رقم الإيداع: ١٤٤٦/١٤١٦٨
ردمك: ٩-٦٣-٨٥٠٦-٦٠٣-٩٧٨

مطبوعات قاصد الحرمين الشريفين
**Guzurin Manufata Masallatai Biyu Masu Alfarma**

**Bugu na farko**
**١٤٤٦هـ/٢٠٢٥م**

**DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINƘAI**

بسم الله الرحمن الرحيم

# Gabatarwar Hukumar Masallatai Biyu Masu Alfarma

Dukkan yabo ya tabbata ga Allah, tsira da amincin Allah su tabbata ga Manzon Allah, da Alayensa da Sahabbansa, da waɗanda suka bi bayansu, bayan haka:

Haƙiƙa Allah Maɗaukaki Ya sanya Ka'aba mai alfarma a matsayin alƙibla wacce zukatan musulmi da jukkunansu ke haduwa zuwa gare ta, kuma ya mai da ita shiriya ga talikai, kuma Harami amintacce. Girmama ta yana gyara rayuwar mutane a cikin al'amuransu na duniya da na Lahira.

A kowace shekara, miliyoyin Musulmi ne ke zuwa Ƙasa mai tsarki, suna ɗauke da burikansu, da niyyoyinsu, da burace-buracensu. Haka nan kuma suna zuwa da tambayoyinsu game da abin da ya wajaba a kansu dangane da addininsu, da abin da ya shige musu duhu a ibadunsu da mu'amalolinsu.

Daga wannan mahangar, girmama Masallacin Harami da girmama mazaunansa da waɗanda ke ziyartar sa ya zama wajibi kuma nauyi mai girma wanda Hukumar Kula da Harkokin Addini a Masallacin Mai Alfarma da Masallacin Annabi ta ɗauka tare da gudanar da shi yadda ya dace.

Wannan aiki mai taken "Guzurin manufatan Masallatai biyu masu alfarma" hujja ce da ke bayyana yadda mutanen wannan ƙasa mai albarka da masu hidima ga Ɗakin Allah mai tsarki suke nuna soyayya da kulawa ga baƙin Allah Mai rahama. Haka kuma, yana zama kyauta mai daraja da maziyarci zai ɗauka tare da shi, yana alfahari da ita yayin da ya koma ƙasarsa.

Hakika "Hukumar Kula da Harkokin Addini a Masallacin Mai Alfarma da Masallacin Annabi", yayin da take miƙa wannan ƙaramin littafin jagora ga 'yan'uwanmu baƙin Allah Mai rahama, wanda ya ƙunshi bayanin yadda ake gudanar da Umara da rukunnanta, da wajibanta, da sunnoninta, da abubuwan da suka haramta yayin Ihrami, tare da ambaton wasu zaɓaɓɓun addu'o'i don Musulmi ya shagaltu da su yayin gudanar da Umara, tana fatan 'yan'uwanmu Musulmi za su fahimci Addininsu, su gode wa Ubangijinsu Mai girma da ɗaukaka, wanda ya sauƙaƙa musu ziyartar wannan Ɗaki mai girma da gudanar da Ibadunsu cikin kwanciyar hankali da sauƙi.

Allah Ya karɓi kyawawan ayyukanmu, kuma dukkan yabo ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai. Tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabinmu Muhammadu, da Alayensa, da sahabbansa, kuma Ya yi daɗin aminci a gare su.

**Hukumar Kula da Harkokin Addini a Masallaci Mai Alfarma da Masallacin Annabi**

# Gabatarwa

Dukkan yabo ya tabbata ga Allah, muna gode Masa, Kuma muna neman taimakonSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharroran kawunanmu da munanan ayyukanmu, duk wanda Allah Ya shiryar babu mai ɓatar da shi, duk wanda kuma Ya ɓatar babu mai shiryar da shi. Kuma ina shaidawa lallai babu abin bauta bisa cancanta sai Allah, Shi kaɗai ba Shi da abokin tarayya, kuma ina shaidawa lallai Annabi Muhammadu BawanSa ne kuma ManzonSa.

Bayan haka:

Lura da kwaɗaituwar Ma'aikatar harkokin Addini na Masallaci mai alfarma da Masallacin Annabi na gyara aikin maniyyata, da taimakekeniya a kan ayyukan nagarta da taƙawa, da yaɗa ilimi, Hukumar ta yi kwaɗayin buga wannan littafi don ya zama mai taimaka wa maziyarta da masu Umara wajen gudanar da ibardarsu a bisa tsarin Alƙur'ani da Sunna, da maganar Ma'abota ilimi.

Wannan taƙaitaccen littafi ne, mai ɗumbin fa'ida game da Umara da hukunce-hukuncenta, kuma saboda kasancewar Umara an shar'anta yin ta a kowane lokaci cikin shekara, sannan Buƙatar sanin hukunce-hukuncenta da siffarta buƙata ce mai sabuntuwa da ba ta yankewa, saɓanin aikin Hajji da yake da lokaci da zamani ƙayyadadde, sai muka ga dacewar rubuta wannan littafin a kan Umara, tare da shi kuma akwai addu'o'i daga Alƙur'ani da ingantacciyar Sunna.

Muna roƙon Allah Ya sanya albarka a wannan aiki, kuma Ya sanya an rubuta shi don neman yardarShi, kuma ya zamo mai amfani ga bayinSa Musulmi.

Daɗin tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabinmu Muhammadu.

# MIƘATAI DA ƊAUKAN HARAMA

Miƙati shi ne guraren da ya wajaba a ɗauki harama daga gare su ga duk mai nufin yin umara.

Kuma Sunna ta iyakance wasu wurare waɗanda bai halatta ga mai nufin yin umara ya wuce ba face sai ya ɗauki harama, adadin miƙatin guda biyar ne.

**Zul hulaifa:** kuma ana kiransa da abyar Ali a yanzu, shi ne miƙatin mutanen Madina da kuma wanda ya bi ta wajen cikin ƴan wasu garuruwan, nisansa da makka ya kai kimanin kilo mita (420).

**Aljuhfa:** wani ƙauye ne kusa da rabig, shi ne miƙatin mutanen sham da misra da magrib da kuma wasunsu da suke bi ta wajen, nisansa da Makka ya kai kimanin kilo (186) amma mutane daga rabig suke ɗaukan harama.

**Ƙarnul Manazil:** Ana kiranshi da Sailul-kabir, shi ne miƙatin mutanen Najd da mutanen Ɗa'ifa da wasunsu da suke bi ta wajen, nisansa da Makka ya kai kimanin kilo (78), Wadi Mahram kuma yana saitinshi, shi ne yake saman Ƙarnul Manazil daga ɓangaren hanyar Hada, nisansa da Makka ya kai kimanin kilo (75).

**Yalamlam:** shi ne miƙatin mutanen Yaman, da waɗanda suka bi ta wajen, nisansa da Makka ya kai kimanin kilo (120).

**Zatu Irƙ:** Ana kiran shi da Darbiya a yanzu, shi ne miƙatin mutanen Iraƙi da waɗanda suka bi ta wajen, nisansa da Makka ya kai kimanin kilo (100).

Wanda kuma gidansa yake gaban waɗannan Miƙatan, to, zai yi haramar Hajji da kuma Umara ne daga gidansa, sai dai wanda gidansa ya kasance a cikin Makka, to, shi zai fita wajen iyakar harami ayayin ɗaukar haramar Umara, amma Hajji kuma sai mutanen Makka su ɗauki haramarsa daga gidanjensu da masauƙinsu.

# TAMBIHI

Duk wanda ya zo ta hanyar sama alhali yana nufin yin Hajji ko Umara, to, ya wajaba a kansa ya ɗauki haramar Umara a cikin jirgi idan ya zo daidai saitin ɗaya daga cikin Miƙatan, ba ya halatta ya jinkirta ɗaukar harama har sai ya sauka a filin jirgin Jidda; saboda ita Jidda ba Miƙati ba ce sai dai ga mazaunanta kaɗai.

Idan ya kasance ba shi da kayan ɗaukan harama; to, sai ya bar wandonsa ya cire riga, sai ya yafa ta a kan kafaɗunsa da ƙirjinsa, sai ya ƙulla niyyar harama, idan ya sauka a filin saukar jirgi sai ya sanya tufafin harama da isowarsa ya kuma cire wandon.

Amma ita mace, bata da wani ƙayyadadden tufafi na ɗaukan harama, don haka sai ta ɗauki haramarta a cikin jirgi tana sanye da kayanta, idan kuma ta kasance ta sanya abun rufe fuska ko niƙabi ko safukan hannu, to, lallai za ta cire su, amma za ta dinga rufe fuskarta da himar ɗinta a yayin haɗuwarta da maza waɗanda ba muharramanta ba.

# RUKUNAN UMARA DA WAJIBANTA DA SUNNONINTA

**RUKUNAN UMARA:**

1. Niyyar fara aikin Umara, kuma ita ce: Ɗaukar harama.

2. Ɗawafi a Ka'aba.

3. Sa'ayi tsakanin dutsen Safa da dutsen Marwa.

Duk wanda ya bar wani rukuni cikin rukunan Umara, to, lallai Umararsa ba ta inganta ba, har sai ya yi ta a bisa sifa ta Shari'a.

**WAJIBAN UMARA:**

- Ɗaukar harama daga Miƙati ga wanda ya bi ta wajenshi. Wanda kuma gidanshi ya zama yana gaba da Miƙati, to, sai ya ɗauki harama a wajen da ya taso. Mazaunin Makka kuma dole ne ya fita wajen harami idan zai ɗaukin haramar Umara.
- Aski ko kuma saisaye.
- Duk wanda ya bar wani wajibi cikin wajiban Umara, idan da gangan ya aikata haka, to, ya aikata zunubi, kuma dole ya yi Fidiya (Fansa), idan kuma ba da gangan ya yi ba, to, Fidiya (Fansa) kawai zai yi.

**SUNNONIN UMARA:**

- Duk abin da ba ya cikin rukunai da wajiban Umara, to, yana cikin sunnoni, kamar yaye kafaɗa da sassarfa yayin Ɗawafi.
- Duk wanda ya bar wata Sunna babu komi a kanshi, amma dai lada ya kuɓuce masa.

# ABUBUWAN DA AKA HARAMTA WA WANDA YA ƊAU HARAMA

Abubuwan da aka hana sun kasu kashi uku:

**Na farko:** Abubuwan da aka haramta wa maza da mata:

1. Ba ya halatta ga maniyyaci bayan niyyar ɗaukan harama ya yanke wani abu na gashinsa da faratansa.
2. Wanda ya ɗau harama dole ne ya nisanci turare da nau'ukansa gabaɗaya.
3. Ba ya halatta sanya safar hannu.
4. Wanda ya ɗau harama ba zai nemi aure ba, kuma ba zai ɗaura wa kansa ko waninsa aure ba.
5. Ya haramta ga wanda ya ɗau harama ya yi jima'i, ko abubuwan da suke jawo a yi shi.
6. Ba ya halatta ya far wa abin farauta na tudu don kashe shi ko zaburar da shi, ko ya yi taimako a kan hakan matuƙar ya ɗau harama.

**Abu na biyu:** Abubuwan da aka hana maza ban da mata:

1. Ba ya halatta sanya ɗinakakken tufafi a bisa yanayinsa da aka rarraba shi.
2. Ba ya halatta a rufe kai da abin da ke ɗamfaruwa da shi, kamar rawani da makamantansa.

**Abu na uku:** Abubuwan da aka hana mata ban da maza:

1. Ba ya halatta ga mace ta rufe fuskarta da niƙabi ko makamancinsa, amma za ta iya suturce fuskarta da himar ɗinta ko wani abu makamancinsa daga maza da ba muharramai ba.

HUKUNCIN WANDA YA AIKATA WANI ABU CIKIN HARAMTATTUN ABUBUWA

- Idan mutum ya aikata wani abu da aka haramta a bisa rashin sani, ko mantuwa, ko tursasawa, to, babu laifi a gare shi kuma babu Fidiya (Fansa).
- Idan kuma ya aikata wani abu da aka haramta don wata buƙata, to, hakan ya halatta a gare shi, amma akwai Fidiya (Fansa) a kansa.
- Idan kuma ya aikata abun da aka haramta ba tare da wani uzuri ko buƙata ba, to, shi mai laifi ne, kuma akwai Fidiya (Fansa) a kansa.

# KASHE-KASHEN ABUBUWAN DA AKA HARAMTA TA FUSKAR FIDIYA (FANSA)

**Abu na farko:** Yanke gashi da farce, da taɓa turare, da sanya safar hannu, da sanya ɗinkakken tufafi ga namiji, da rufe kansa, da sanya niƙabi ga mace, da runguma saboda sha'awa, a cikin kowane ɗaya daga waɗannan abubuwa da aka haramta an ba da zaɓi ga wanda ya yi su tsakanin abubuwa guda uku:

a. Azumtar kwanaki uku a jere, ko a rarrabe.

b. Ko ciyar da miskinai guda shida, za a ba wa kowane miskini rabin Sa'i na abinci, kamar dabino, ko shinkafa, ko wani abu da ba su ba.

c. Ko kuma yanka ƙaramar dabba (Dangin tumaki ko awaki), da raba namanta ga miskinan Harami.

**Abu na biyu:** Wanda ya bar wajibi cikin wajiban Umara, kamar ɗaukar harama daga Miƙati, to, wajibi ne a kansa ya yanka dabbar Fidiya (Fansa), wacce za a iya yin layya da ita, wato na miji ko macen rago, ko taure, sai ya raba naman gabaɗaya ga talakawan Harami, kuma ba zai ci komai daga gare shi ba.

**Abu na uku:** Fansar jima'i: Duk wanda ya yi jima'i kafin Sa'ayi, to Umararsa ta lalace, kuma dole ya kammala ta, sannan ya rama ta, tare da yin Fidiya (Fansa), idan hakan bai samu ba, sai ya yi azumin kwana goma.

Wanda kuma ya yi jima'i bayan Sa'ayi, kafin ya yi aski ko saisaye, to, Umararsa ba za ta lalace ba, amma zai yanka dabbar

fansa, idan hakan bai samu ba, sai ya yi azumin kwana goma.

**Abu na huɗu:** Kaffarar farauta, kuma yana da yanayi biyu:

- Idan dabbar da aka farauto tana da makamanciyarta a dabbobin gida, to, za a ba da zaɓi tsakanin abubuwa guda uku:

a. Imma a yanka makamanciyarta, sannan a raba ta tsakanin talakawa da miskinai a Makka.

b. Ko kuma a duba nawa ne ƙimar kuɗin wannan makamanciyar, sai ya sayi abinci da shi, sannan ya raba shi ga miskinai, kowane miskini za a ba shi rabin Sa'i na abinci.

c. ko kuma ya yi azumin yini ɗaya a maimakon kowane miskini.

- Idan kuma dabbar da aka farauto ba ta da makamanciya a dabbobin gida, kamar fari, to, za a ba shi zaɓi tsakanin abubuwa guda biyu:

a. Ko dai a duba nawa ne ƙimar kuɗin abin da aka farauto, sai a ba da abinci da ya yi daidai da wannan kuɗin wanda za a raba shi tsakanin miskinai, kowane miskini a ba shi rabin Sa'i.

b. ko kuma ya yi azumin yini ɗaya a maimakon kowane miskini.

# YADDA AKE UMARA

- Lokacin da maniyyacin Umara ya isa Miƙati:
  - Mustahabbi ne yin wanka da sanya turare kafin saka Ihrami.
  - Namiji zai sanya gyauto da kwarjalle (Zane da mayafi), kuma mustahabbi ne su zama farare tsaftatattu.
  - Amma ita mace ya halatta a gare ta ta yi Ihrami da abin da ta ga dama na tufafi mai suturcewa, amma ba za ta saka niƙabi ko safar hannu ba.
  - Sai mutum ya yi niyyar fara Umara a zuciyarsa, kuma an Shar'anta masa furta abin da ya niyyata a zuciyar tashi, sai ya ce: (Labbaika Umratan), ko kuma (Allahumma labbaika Umratan).
  - Idan wanda ya ɗauki harama ya ji tsoron kada ya gagara yin Umararsa saboda kasancewarsa mara lafiya ko yana tsoron abokan gaba da makamantan haka; to, mustahabbi ne ya ce a lokacin da zai ɗau harama: (Fa in habasani habisun; fa mahalli haisu habastani). Kuma fa'idar wannan sharaɗi shi ne cewa maniyyaci idan wani abu da zai hana shi kammala Umararsa ya bijiro masa, ya halatta a gare shi ya yi tahalluli (wato ya katse Umarar tashi), kuma babu komai a kansa.
  - Mustahabbi ne yawaita Talbiya, da ɗaga murya da ita a kan hanyar zuwa Makka.
- Abin da mai Umara zai aikata lokacin shigarsa Masallaci mai alfarma:

- Idan ya iso Masallaci mai alfarma, an sunnanta masa gabatar da ƙafar dama kafin hagu lokacin shiga, sai kuma ya ce: «Bismillahi, wassalatu wassalamu ala rasulillahi». Ibnu Maja ne ya rawaito, «A'uzu billahil-Azim, wa bi wajhihil-karim, wa sulɗanihil-ƙadim, minash-shaiɗanirrajim». Abu Dawuda ne ya rawaito, «Allahummaftah li abwaba rahmatika». Muslim ne ya rawaito.

- Sai ya tafi wajen Alhajarul-aswad don ya fara Ɗawafi, sai ya taɓa Alhajarul-aswad da hannunshi na dama, sannan ya sumbace shi idan ya samu daman hakan, idan kuwa bai samu dama ba, sai ya sumbaci hannun nasa idan har ya taɓa dutsen da shi, idan kuma bai samu daman taɓa dutsen da hannun nasa ba, to, ya fuskanci dutsen, sai ya yi nuni izuwa gare shi da hannunsa, ya yi kabbara, kada kuma ya sumbaci hannun, kuma abin da ya fi shi ne ka da ya yi turereniya don kada ya cutar da mutane, shi ma ya cutu.

- Kuma zai ce a lokacin taɓa dutsen: «Bismillahi, Wallahu Akbar».

- Sannan sai ya bi ta gefen dama, ya sanya Ka'aba a hagunsa, idan ya isa kusurwar Arruknul yamani sai ya taɓa shi ba tare da ya sumbace shi ko ya yi nuni gare shi ba, kuma ba zai yi kabbara ba, ba zai shiga turmutsitsi don taɓa shi ba, kuma zai riƙa cewa a tsakanin kusurwa biyun abin ya tabbata daga Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi: **(Rabbana atina fiddunya hasatan wa fil'akhirati hasanatan wa ƙina azaban nar)**. (Suratul Baƙara: 201).

- Yaye ƙafaɗa daga farkon fara Ɗawafi har zuwa ƙarshensa, sifarshi kuma ita ce: Yaye kafaɗar dama, idan ya gama Ɗawafi sai ya rufe kafaɗunsa biyu duka.
- Sassarfa a zagaye uku na farko kawai, wato sauri wajen tafiya tare da kusantuwar taku.
- Idan ya gama zagaye bakwai na ɗawafi, sai ya tafi wajen Maƙamu Ibrahim idan ya samu dama, sannan ya yi Salla raka'a biyu, zai karanta Fatiha da Suratul Kafirun a raka'ar farko, a ta biyu kuma sai ya karanta Fatiha da Ƙulhuwallahu.
- Sannan idan ya idar da Sallar, mustahabbi ne ya sha ruwan Zamzam idan ya samu dama, sannan ya tafi izuwa ga Alhajarul aswad ya taɓa shi da hannunsa idan ya samu daman hakan.
- Sannan ya tafi wajen dutsen Safa ya hau kan shi, idan ya kusanto shi sai ya karanta: **(Innassafa walmarwata min sha'a'irillahi, faman hajjal baita awi'tamara fala junaha alaihi an yaɗɗauwafa bihima, faman taɗauwa'a khairan fa'innallaha shakirun alim)**. (Suratul Baƙara: 158).
- Zai karanta wannar aya idan ya kusanto dutsen Safa kafin ya hau kan dutsen, kuma ba zai karanta ta ba sai a wannan waje, kuma a farkon zagayen farko kaɗai, sannan ba zai maimaita karanta ta a sauran Zagayen ba.
- Sannan ya hau saman dutsen Safa har sai ya ga Ka'aba, sai ya fuskance ta ya ce: (Allahu Akbar), ya kuma ɗaga hannayensa biyu, sai ya gode wa Allah ya yi addu'a. Haƙiƙa an rawaito daga Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yana cewa a wanna wuri: **(La'ilaha illallahu wahdahu la sharika**

**lahu, lahulmulku wa lahulhamdu, wa huwa ala kulli shai'in ƙadir, la'ilaha illallahu Wahdahu, anjaza wa'dahu, wa nasara abdahu, wa hazamal'ahzaba wahdahu)**, zai maimaita wannan Zikiri sau uku, sai ya yi addu'a a tsakanin haka da abin da yake so.

- Sannan sai ya sauka daga dutsen Safa yana mai nufatan dutsen Marwa, yana mai tafiya a nutse, yana ambaton Allah yana addu'a wa kansa da iyalansa da masoyansa har sai ya isa farkon layi mai koren haske, sai ya yi gudu sosai gwargwadon yanda zai iya, har sai ya isa Ƙarshen koren hasken, sannan ya cigaba da tafiya a tsanake har sai ya je ya hau kan dutsen Marwa, idan ya isa wajen dutsen Marwa ya hau kanta sai ya fuskanci Alƙibila, sai ya yi irin yanda ya yi a kan dutsen Safa.
- Sai ya yi sa'ayi sau bakwai, daga dutsen Safa zuwa dutsen Marwa zagaye ɗaya ke nan, daga dutsen Marwa zuwa dutsen Safa zagaye na biyu ke nan, idan ya zo wajen alamu biyu masu koran haske sai ya yi gudu sosai, amma kada ya cutar da na gefensa, haka zai tayi har sai ya kamala zagaye bakwai.
- Sannan sai ya aske kansa, ko ya saisaye shi, ita kuma mace sai ta haɗa gashinta ta yanki gwargwadon saman yatsa.

• Daga nan shi kenan ya gama Umara, kuma duk abin da aka haramta masa bayan ɗaukar harama ya halatta gare shi.

Daɗin tsira da aminci su tabbata ga Annabinmu Muhammadu da Alayensa da Sahabbansa gabaɗaya.

# ZAƁAƁƁUN ADDU'O'I

- Allahumma, lakal-hamdu, hamdan kasīran ɗayyiban mubarakan fīh, kamā tuḥibbu Rabbānā wa tarḍā, hamdan lā yanƙaɗiʿu wa lā yabīdu, wa lā yafna, mil'a samāwātika, wa mil'a arḍika, wa mil'a mā shi'ita min shai'in baʿadu, ʿadada mā ḥamadakal-ḥāmidūn, wa ʿadada mā ghafala ʿan zikrikal-ghāfilūn, was-ṣalātu was-salāmu ʿalā ʿabdika wa rasūlika Muḥammadin, khātamin-nabiyīna wa rusulika, wa khiratika min Khalƙika, wa amīnika ʿalā wahyika, wa ʿalā ālihi wa ṣaḥbihi ajmaʿīn.

Ya Allah dukkan yabo naKa ne, yabo mai yawa, mai Kyawu, mai albarka, kamar yadda Kake so ya Ubangi-jinmu kuma Ka yarda, yabon da ba ya yankewa, baya bacewa, kuma baya ƙarewa, cikin sammanKa, kuma cikin ƙasarKa, kuma cikin abin da Kake so bayansu, yawan adadin yabon da masu yabo suka Maka, da adadin gafalar da gafalallu suka yi daga barin anbatonKa, salati da Sallama su tabbata ga BawanKa kuma ManzonKa Muhammadu, cikamakon AnnabawanKa da Manzan-ninKa, zaɓaɓɓe cikin halit-tunKa, kuma Amintacce a kan wahayinKa, da Alayensa da Sahabbansa gabaɗaya.

- Allahumma, lakal-hamdu, anta nūrus-samāwāti wal-arḍi wa man fīhinna, wa lakal-hamdu, anta ƙayyūmus-samāwāti wal-arḍi wa man fīhinna, wa lakal-hamdu, antal-ḥaƙƙu, wa waʿduka ḥaƙƙun, wa ƙauluka ḥaƙƙun, wa Liƙa'uka ḥaƙƙun, wal-jannatu ḥaƙƙun, wan-nāru ḥaƙƙun, was-sāʿatu ḥaƙƙun,

wan-nabiyyūna ḥaƙƙun, wa Muḥammad Sallalahu alaihi wa Salla-ma ḥaƙƙun.

Ya Allah dukkan yabo naKa ne, Kai ne hasken sammai da ƙasa da waɗanda ke cikinsu, dukkan yabo naKa ne, Kai ne tsayayye a kan sammai da ƙasa da waɗanda ke cikinsu, dukkan yabo naKa ne, Kai ne Gas-kiya, kuma alƙawarinKa gaskiya ne, maganarKa gas-kiya ce, haɗuwa da Kai gaskiya ne, Aljanna gaskiya ce, wuta ma gaskiya ce, tashin Alƙiyama gaskiya ne, Annabawa gaskiya ne, kuma Muhammadu tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi shi ma gaskiya ne.

- Allahumma, laka aslamtu, wa alaika tawakkaltu, wa bika āmantu, wa ilaika anabtu, wa bika khāṣamtu, wa ilaika ḥākamtu, faghfir lī mā ƙaddamtu wa mā akhkhartu, wa mā asrartu wa mā aʿlantu, antal-muqaddimu, wa antal-mu'akhkhir, lā ilāha illā anta, wa lā ḥaula wa lā quwwata illā billāhil-ʿaliyyil-ʿaẓīm.

Ya Allah gare Ka na miƙa wuya, da Kai nake dogaro, da Kai na yi Imani, gare Ka nake komowa, gare Ka nake kai husuma, gare Ka nake kai ƙara, Ka gafarta mun abin da na gabatar na laifi, da abin da ma zan yi daga baya, da abin da na ɓoye, da abin da na bayyana, Kai ne Mai gabatarwa, kuma Kai ne Mai jinkirtawa, babu abin bauta bisa cancanta sai Kai, kuma ba ni da wata dabara ko ƙarfi sai da Allah Maɗaukaki Mai girma.

- Allahumma Atí Nafsí Taƙwahá, Wazakkihá An-ta Khairu Man Zakkáhā, Anta Walíyyuhá Wa Mawláhā.

Ya Allah, Ka ba wa zuciyata ta tsoronKa, Ka tsarkake ta, Kai

ne mafi alherin Mai tsarkaketa, Kai ne Majiɓincinta kuma Jagoran-ta.

- Allahumma Inní A'údhu Bika Min 'Ilmin Lā Yanfa'u, Wa Min Ƙalbin Lā Yakhsha'u, Wa Min Nafsin Lā Tashba'u, Wa Min Da'watin Lā Yustajābu Lahā.

Ya Allah, ina neman tsarinKa daga ilimi mara amfani, da zuciyar da ba ta jin tsoronKa, da rai wanda ba ya gamsuwa, da kuma addu'ar da ba a karɓa.

- Allahumma Inní As'aluka Bi'Anna Lakal Hamdu, Lā Ilāha Illā Anta, Badī'as Samāwāti Wal Arḍi, Yā Dhāl Jalāli Wal Ikrām, Yā Ḥayyu Yā ƙayyūm, An Taghfira Lí Watarḥamaní, Wa Idhā Aradta Biƙaumin Fitnatan Faƙbiḍní Ilaika Gaira Maftūnin.

Ya Allah, ina roƙon Ka saboda lalle yabo ya tabbata gare Ka, babu abin bautawa bisa cancanta sai Kai, ya Maƙagin sammai da ƙasa, ya Mai girma da karamci, Ya Rayayye, Ya Tsayayye, Ka gafarta min kuma Ka yi min rahama, idan kuma Ka nufi wasu mutane da wata fitina, to Ka karɓi raina zuwa gareKa ba tare da an jarabce ni ba.

- Rabbana Atiná FidDunyá Ḥasanatan, Wa Fil Ākhira-ti Ḥasanatan, Wa ƙinā 'Azaban Nār.

Ya Ubangijinmu, Ka ba mu alheri a duniya da Lahira, Ka tsare mu daga azabar wuta.

- Rabbana Āmannā Faghfir Lanā Warḥamnā, Wa An-ta Khairur Rāḥimīn.

Ya Ubangijinmu, mun yi Imani, don haka Ka gafarta mana kuma Ka yi mana ra-hama, Kai ne mafi alherin masu rahama.

- Rabbana Lā Tuzigh ƙulūbanā Ba'ada Idh Ha-daitanā Wa hab Lanā Min Ladunka Raḥmatan, In-naka Antal Wahhāb.

Ya Ubangijinmu, kada Ka karkatar da zukatanmu bayan Ka shiryar da mu, kuma Ka ba mu rahama daga gare Ka, lallai Kai ne Mai yawan kyauta.

- Rabbana Lā Tu'ākhidhnā In Nasīnā Au Akhɗa'anā, Rabbana Wa Lā Taḥmil 'Alainā Isran Kamā Ḥamaltahu 'Alāl Ladhīna Min ƙablinā, Rabbana Wa Lā Tuḥammilnā Mā Lā ɗāƙata Lanā Bihi, Wa'afu 'Annā Waghfir Lanā Warḥamnā, Anta Maulānā Fānṣurnā 'Alāl ƙaumil Kāfirīn.

Ya Ubangijinmu, kada Ka kama mu da laifi idan mun yi Mantuwa ko mun yi kusku-re, Ya Ubangijinmu, kada Ka ɗora mana wani nauyi irin wanda ka ɗora wa waɗanda suke gabaninmu, Ya Ubangijinmu, kada kuma Ka ɗora mana abin da ya fi ƙarfinmu, kuma Ka yafe mana, kuma Ka gafarta mana, kuma Ka jiƙan mu. Kai ne Majiɓincin lamuranmu, don haka Ka taimake mu akan mutane kafirai.

- Rabbij alní Muƙīmas Ṣalāti Wa Min Dhurriyyatí Rabbana Wataƙabbal Du'ā', Rabbanag fir Lí Wa li walidaiya Wa lil Mu'minīna Yauma Yaƙūmul Ḥisāb.

Ya Ubangijina, Ka sanya ni mai tsayar da Salla ni da zur-iya ta, Ya Ubangijinmu, Ka karɓi addu'ata. Ya Ubangijinmu, Ka gafarta min da iyayena da muminai a ranar da hisabi zai kankama.

- Rabbana Hablana Min Azwājinā Wa Dhurriyyātinā ƙurrata A'ayunin Waj'alnā LilMuttaƙīna Imāmā.

Ya Ubangijinmu, Ka ba mu masu faranta mana daga matayanmu da zuriyarmu, Ka sanya mu abin koyi ga masu tsoron Ka.

- Rabbana Ātinā Min Ladunka Raḥmatan Wa Haiyi'i Lanā Min Amrinā Rashadā.

Ya Ubangijinmu, Ka ba mu rahama daga gare Ka, Ka kuma tanadar mana da shiriya cikin lamarinmu.

- Rabbana Wa Ātinā Mā Wa'adtanā 'Alā Rusulika Wa Lā Tukhzinā Yaumal ƙiyāma, Innaka Lā Tukhil-ful Mī'ād.

Ya Ubangijinmu, Ka ba mu abin da Ka yi mana alƙawari ta wurin ManzanninKa, kada Ka kunyata mu a ranar Alƙiyama, lallai Kai ba Ka saɓa alƙawari.

- Allahumma Inní As'alukal Hudá, Wat Tuƙá, Wal Afāfa, Wal Ghiná.

Ya Allah, ina roƙon Ka shiriya, da tsoronKa, da kamewa, da wadatar zuci.

- Allahummaƙsim Lí Min Khashyatika Mā Taḥūlu Bihi Bainí Wa Baina Ma'ṣiyatika, Wa Min ɗā'atika Mā Tuballighunī Bihi Jannataka, Wa Minal Yaƙīni Mā Tuhauwinu Bi-hi 'Alaiya Maṣā'ibad Dunyā, Wa Matti'inī Bi sam'i, Wa Baṣarī, Wa ƙuwwatí Abadan Mā Abƙaitaní, Waj'alhul Wāritha Minní, Waj'al Tha'arí 'Alá Man zalamani, Wānṣurní 'Alá Man 'Ādāní, Wa Lā Taj'al Muṣībatí Fí Dīnī, Wa Lā Taj'alid Dunyā Akbara Hammí, Wa Lā Mablagha 'Ilmī, Wa Lā Ilán

Nāri Maṣírí, Waj'alil Jannata Hiya Dāri, Wa Lā Tusalliɗ 'Alaiya Bi Dhunūbí Man Lā Yakhāfuka, Wa Lā Yarḥamuní Bi rahmatiKa Ya Arhamar Rahimin.

Ya Allah, Ka sa min tsoronKa wanda zai zama shinge tsakanina da saɓonKa, da biyayyarKa wadda za ta kai ni zuwa aljannarKa, da yaƙini wanda zai sauƙaƙa min jarabawar duniya. Ka amfanar da ni da ji na, da gani na, da ƙarfi na har tsawon lokacin da Ka rayar da ni, Ka sa na ci gajiyarsu tsawon rayuwa ta. Ka ɗauki fansa daga wanda ya zalunce ni, Ka taimake ni akan maƙiyina. Kada Ka sanya musifata ta kasance acikin addinina, kada Ka sanya duniya ta zamto babbar damuwata ko iyakar sani na, kuma kada Ka sanya makomata ta zamanto ita ce wuta. Ka sanya aljanna ita ce makomata. Kada Ka damƙa ni ga wanda baya tsoronKa kuma baya jinƙai na sakamakon laifina, da rahamarKa, Ya Mafi rahamar masu Rahama.

- Allahumma Inní A'údhu Bi'izzatika Lā Ilāha Illā Anta An Tuḍillaní, Antal Ḥayyul Ladhí Lā Yamūtu, Wal Jinnu Wal Insu Yamūtūn.

Ya Allah, ina neman tsari da buwayarKa — babu abin bautawa bisa cancanta sai Kai — kada Ka ɓatar da ni. Kai ne Rayayye wanda ba ya mutuwa, alhali dukkan aljannu da mutane suna mutuwa.

- Allahumma Fāɗiras Samāwāti Wal Arḍi, 'Āli-mal Ghaibi Wash Shahādah, Lā Ilāha Illā Anta, Rabba Kulli Shai'in Wa Malikahu, A'ūdhu Bi-ka Min Sharri Nafsí, Wa Min Sharrish

Shaiɗāni Wa Shirkihi, Wa An Aƙtarifa ‘Alá Nafsí Sū’an, Au Ajur-rahu Ilá Muslimin.

Ya Allah, Maƙagin sammai da ƙasa, Masanin abin da ke fili da na ɓoye, babu abin bautawa bisa cancanta sai Kai, Ubangijin komai kuma Mamallakinsa, Ina neman tsarinKa daga sharrin kaina, da sharrin shaiɗan da waswasinsa, da kuma aikata wa kaina abu marar kyau, ko jan hakan zuwa ga wani Musulmi.

- Allahumma Aṣliḥ Lí Dīnī AlLadhí Huwa ‘Iṣmatu Amrī, Wa Aṣliḥ Lí Dunyāyal Latī Fíha Ma‘āshí, Wa Aṣliḥ Lí Ākhiratíl Latī Ilaiha Ma‘ādí, Waj‘alil Ḥayāta Ziyādatan Lí Fí Kulli Khairin, Waj‘alil Mauta Rāḥatan Lí Min Kulli Sharrin.

Ya Allah, Ka gyara min addini na wanda shi ne katangar al’amurana, Ka gyara min duniyata wacce a cikinta nake rayuwa, Ka gyara min lahirata wacce ita ce makoma ta. Ka sanya rayuwa ta zama ƙari a gare ni a cikin kowane alheri, Ka sanya mutuwa ta zama hutu a gare ni daga kowane sharri.

- Allahumma Inní As’alukal ‘Āfiyah Fíd Dunyā Wal Ākhirah, Allahumma Inní As’alukal Afwa Wal Āfi-yah Fí Dīnī, Wa Dunyāya, Wa Ahlí, Wa Mālí, Al-lahummas tur ‘Auratí, Wa Āmin Rau‘ātí.

Ya Allah, ina roƙon Ka lafiya a duniya da Lahira, Ya Allah, ina roƙon Ka afuwa da lafiya a addinina da rayuwata da iyalina da dukiyata. Ya Allah, Ka suturta min al’aurata, Ka amintar da ni daga firgici.

- Allahummah faẓní Min Baini Yadaiya Wa Min Khalfī, Wa ‘An Yamíní Wa ‘An Shimālí, Wa Min Fauƙí, Wa A‘ūdhu Bi‘aẓamatika An Ughtāla Min Taḥtí.

Ya Allah, Ka kiyaye ni daga gaba na da baya na da dama na da hagu na da kuma sama na, ina neman tsari da girmanKa kada a shammace ni ta ƙasa na.

- Allahumma Aḥsin ʻĀƙibatí Fíl Umūri Kullihā, Wa Ajirní Min Khizyid Dunyā, Wa ʻAdhābil Ākhirah.

Ya Allah, Ka kyautata ƙarshen al'amurana gabaɗaya, Ka tsare ni daga kunya ta duniya, da azabar Lahira.

- Allahumma Aʻinní ʻAlá Dhikrika, Wa Shukrika, Wa Ḥusni ʻIbādatika.

Ya Allah, Ka taimake ni wajen ambatonKa da godiyarKa da kyautata bautarKa.

- Allahumma Inní Aʻūdhu Bika Min Zawāli Niʻmatika, Wa Taḥawwuli ʻĀfiyatika, Wa Min Fu-jā'ati Niƙmatika, Wa Min Jamīʻi Sakhɗika.

Ya Allah, ina neman tsarin-Ka daga gushewar ni'imarKa, da canzawar lafiya da shammatar bala'inKa da kuma dukkan fushinKa.

- Allahumma Innaka ʻAfuwwun Tuḥibbul Afwa; Faʻafu ʻAnnī.

Ya Allah, lalle Kai Mai afuwa ne, Kana son afuwa don haka Ka yafe min.

- Allahumma Inní As'aluka Minal Khairi Kullihi, ʻĀji-lihi Wa Ājilihi, Mā ʻAlimtu Minhu, Wa Mā Lam Aʻlam, Wa Aʻūdhu Bika Minash Sharri Kullihi, ʻĀjilihi Wa Ājilihi, Mā ʻAl-imtu Minhu, Wa Mā Lam Aʻalam.

Ya Allah, ina roƙon Ka alheri duka, na kusa da na nesa, wanda na sani da wanda ban sani ba, kuma ina neman tsari daga dukkan sharri, na kusa da na nesa, wanda na sani da wanda ban sani ba.

- Allahumma Inní As'aluka Min Khairi Mā Sa'alaka Minhu 'Abduka Wa Nabiyyuka Muḥammad Sallallahu alaihi wa Sallam' Wa A'ūdhu Bika Min Sharri Mās ta'ādha Minhu 'Abduka Wa Nabiyyuka Muḥammad Sallallahu alaihi wa Sallam.

Ya Allah, ina roƙon Ka daga alherin abin da BawanKa kuma ManzonKa Muhammadu tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya roƙa, kuma ina neman tsarinKa daga dukkan sharri wanda BawanKa kuma ManzonKa Muhammadu tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya nemi tsari daga gare shi.

- Allahumma Inní As'alukal Jannata, Wa Mā ƙarraba Ilaiha Min ƙaulin, Au 'Amalin, Wa A'ūdhu Bika Minan Nāri, Wa Mā ƙarraba Ilaiha Min ƙaulin, Au 'Amalin.

Ya Allah, ina roƙon Ka Aljanna da duk abin da yake kusantarwa zuwa gare ta na magana ko aiki. Kuma ina neman tsarinKa daga wuta da duk abin da yake kusantarwa zuwa gare ta na magana ko aiki.

- Allahumma Inní As'aluka Mujibāti Raḥmatika, Wa 'Azā'ima Maghfiratika, Wal Ghanīmata Min Kulli Bīrrin, Was Salāmata Min Kulli Ithmin, Wal Fauza BilJannati, Wan Najāta Minan Nār.

Ya Allah, ina roƙon Ka abubuwan da suke jawo rahamarKa, da abubuwan da suke tabbatar da gafararKa, da samun dukkan alheri, da tsira daga kowane zunubi, da rabauta da Aljanna, da kuɓuta daga wuta.

- Allahumma Jannibní Munkarātil Akhlāƙi Wal A'amāli, Wal Ahwā'i Wal Adwā'i.

Ya Allah, Ka nisantar da ni daga munanan ɗabi'u, da ayyuka, da son zuciya, da cututtuka.

- Allahummag fir Lí Dhunūbí Jamī'an, Wahdini Li Aḥsanil Akhlāƙi, Lā Yahdī Li Aḥsaniha Illā Anta, Was rif 'Annī Saiyi'ahā, Lā Yaṣrifu 'Annī Saiyi'ahā Illā Anta.

Ya Allah, Ka gafarta min dukkan zunubaina, Ka shiryar da ni zuwa kyawawan ɗabi'u, babu wanda ke shiryarwa zuwa ga kyawawan ɗabi'u sai Kai. Ka nisantar da ni daga munanan ɗabi'u, babu wanda ke nisantar min da su sai Kai.

- Allahumma Inní As'aluka Khashyatika Fíl Ghaibi Wash Shahāda, Wa As'aluka Kalimatal Ḥaƙƙi Fíl Ghaḍabi War Riḍā, Wa As'alukal ƙasda Fíl Faƙri Wal Ghinā, Wa As'aluka Na'īman Lā Yanfadu, Wa ƙurrata 'Ainin Lā Tanƙaɗi'u, Wa As'alukar Riḍā Ba'adal ƙaḍā'i, Wa Bardal aishi Ba'adal Mauti, Wa Lazzatan Naẓari Ilá Wajhikal Karīm, Wash Shauƙa Ilá Liƙā'ika, Fí Ghairi Ḍarrā'in Muḍirrah, Wa Lā Fitnatin Muḍillah.

Ya Allah, ina roƙon Ka Ka sanya ni na zama mai jin tsoronKa a fili da ɓoye. Ina roƙon Ka maganar gaskiya a yayin fushi da kuma yarda, Ina roƙon Ka daidaito tsakanin talauci da

wadata. Ina roƙon Ka ni'ima mai ɗorewa da farin ciki mara yankewa, ina roƙon Ka yarda bayan hukunci, da kwanciyar hankali bayan mutuwa, ina roƙon Ka ni'imar ganin fus-karKa mai daraja, da ƙaunar gamuwa da Kai ba tare da wata cuta mai cutarwa ko fitina mai ɓatarwa ba.

- Allahumma Zaiyinnā Bi Zīnatil Īmān, Waj'alnā Hudātan Muhtadīn, Ghaira Ḍāllīn, Wa Lā Muḍillīn, Silman Li Auliyā'ika, Ḥarban 'Alá A'adā'ika, Nuḥibbu Biḥubbika Man Aḥabbaka, Wa Nu'ādi Bibaḡḍika Man 'Ādāka, Au Khālafaka.

Ya Allah, Ka ƙawata mu da ado na Imani, Ka sanya mu mu zamto shiryayyu masu shiriya, ba ɓatattu ba, ba kuma masu ɓatarwa ba. Ka sanya mu masu zaman lafiya da masoyanKa, masu yaƙi da maƙiyanKa, ya zamanto Muna ƙaunar wanda ya ƙaunace Ka saboda ƙaunarKa, kuma muna ƙin wanda ya ƙiKa ko ya saɓa Maka.

- Allahumman ƙulní Min Dhullil Ma'aṣiyati Ilá 'Izzatiɗɗa'ah, Wa Aghniní Biḥalālika 'An Ḥarāmika, Wa Bi ɗā'atika 'An Ma'aṣiyatika, Wa Bi Faḍlika 'Amman Siwāka, Yā Ḥayyu Yā ƙayyūm, Yā Dhāl Jalāli Wal Ikrām.

Ya Allah, Ka fitar da ni daga ƙasƙancin saɓo zuwa ɗaukakar biyayya, Ka wadatar da ni da halal ɗinKa daga abin da Ka haramta, Ka kuma wadatar da ni da biyayyarKa daga saɓonKa, da kuma falalarKa daga waninKa. Ya Rayayye, Ya Tsayayye, Ya Ma'abocin girma da karamci.

- Allahumma Inní A'ūdhu Bika Minal Hammi Wal Ḥazan,

Wa Minal Ajzi Wal Kasal, Wa Minal Jubni Wal Bukhli, Wa Minal Ma'athami Wal Maghram, Wa Min Ghalabatid Daini, Wa ƙahrir Rijāl.

Ya Allah, ina neman tsari daga damuwa da baƙin ciki da gazawa da kasala da tsoro da rowa da zunubi da bashi, da kuma rinjayar maƙiya.

- Allahumma Inní A'ūdhu Bika Minal Baraṣi, Wal Junūni, Wal Juzām, Wa Min Sayyi'il Asƙām.

Ya Allah, ina neman tsari daga cutar fata da hauka da kuturta da munanan cututtuka.

- Allahumma Rabbas Samāwāti Wal Arḍi, Wa Rabbal 'Arshil Aẓīm, Rabbana Wa Rabba Kulli Shai'in, Fāliƙal Ḥabbi Wan Nawā, Munzilat Taurāti, Wal Injīl, Wal Furƙān, A'ūdhu Bika Min Sharri Kulli Dhī Sharrin Anta Ākhizunun Bi Nāṣiyatihi.

Ya Allah, Ubangijin sammai da ƙasa Ubangijin Al'arshi mai girma, Ubangijinmu kuma Ubangijin komai, Mai tsaga ƙwaya da ƙwallo, Wanda ya saukar da Attaura da Injila da Alƙur'ani, ina neman tsarinKa daga sharrin duk wani mai sharri, wanda Kai ne Mai riƙe da rayuwarsa.

- Allahumma Antal Auwalu, Fa Laisa ƙablaka Shai'un, Wa Antal Ākhir, Fa Laisa Ba'adaka Shai'un, Wa AntaZ Ẓāhiru, Fa Laisa Fauƙaka Shai'un, Wa An-tal Bāɗin, Fa Laisa Dūnaka Shai'un, Iƙḍi 'Annīd Daina, Wa Aghniní Minal Faƙri.

Ya Allah, Kai ne Na farko, babu wani abu kafinKa, Kai ne Na ƙarshe, babu wani abu bayanKa, Kai ne Bayyananne, babu wani abu a samanKa. Kai ne Ɓoyayye, babu wani abu a ƙasanKa. Ka biya min bashi, Ka wadatar da ni daga talauci.

• Allahumma Anta Rabbí Lā Ilāha Illā Anta, Khalaƙtaní Wa Anā ʻAb-duka, Wa Anā ʻAlá ʻAhdi-ka, Wa Waʻadika Mās taɗaʻatu, Aʻūdhu Bika Min Sharri Mā Ṣanaʻatu, Abū'u Laka Bi Niʻmatika ʻAlaiya, Wa Abū'u Bi zanbi, Fagfir Li Fa innahu La Yagfirudhunuba Illa Anta.

Ya Allah, Kai ne Ubangijina, babu abin bautawa sai Kai. Kai ne Ka halicce ni, ni bawanKa ne. Ina kan alƙawari da yarjejeniyarKa iya iyawata. Ina neman tsari daga sharrin abin da na aikata. Ina tabbatar da ni'imarKa a kaina, kuma ina tabbatar da zunubaina. Don haka Ka gafarta mini, lalle ba mai gafarta zunubai sai Kai.

• Allahumma inni as'aluka fi'ilal khairati, wa tarkal munkarati, wa hubbal Masakini, wa an taghfira li wa tarhamani, wa idha aradta bi ibadika fitnatan faƙbid-ni ilaika ghaira maftunin

Ya Allah! Ina roƙon Ka Ka bani ikon aikata alheri, da barin aikata mummuna, da son talakawa. Ka gafarta min, Ka rahamce ni. Idan Ka yi nufin jarabtar bayinka, Ka karɓi raina gare ka ba tare da an jarabce ni ba.



• Allahumma, inni a'uzu bi-ka min jahdil bala'i, wa darakish shaqa'i, wa su'il qada'i, wa shamatatil a'ada'i.

Ya Allah! Ina neman tsarinka daga wahalar jarabawa, da mummunar kaddara, da dariyar abokan gaba a gare ni.

- Allahumma, ya muqallibal qulubi, thabbit qalbi ala dinika, Allahumma, ya musarrifal qulubi wal ab-sari, sarrif qalbi ala ɗa'atik.

Ya Allah! Ya Mai juya zukata, Ka tabbatar da zuciyata a kan AddininKa. Ya Allah! Ya Mai sarrafa zukata da idanu, Ka karkatar da zuciyata zuwa ga yi Maka biyayya.

- Allahumma, la tada' li zamban illa ghafartahu, wa la hamman illa farrajtahu, wa la dainan illa ƙadaitahu, wa la hajatan min hawa'ijid dunya wal akhirati hiya laka ridan, wa lana fiha salahun illa qadaitaha ya arhamar rahimin.

Ya Allah! Kada Ka bar min wani zunubi face Ka gafarta shi, kuma kada Ka bar min wata damuwa face Ka warware ta, kada Ka bar min wani bashi face Ka biya, kuma kada Ka ba bar min wata buƙata daga cikin buƙatun duniya da Lahira - wadda Ka yarda da su kuma akwai alheri gare mu a cikin ta- face Ka biya su, ya Mafi tausayin masu tausayi.

- Rabbana taqabbal minna innaka antas Sami'ul 'Alim. Wa tub 'alayna innaka antat Tawwabur Rahim.

Ya Ubangijinmu! Ka karɓa daga gare mu, lalle Kai ne Mai ji kuma Masani. Ka karɓi tuba daga gare mu, lalle Kai ne Mai yawan karɓar tuba Mai rahama.

- Rabbana ighfir lana wa li'ikhwaninal ladhina sabaƙuna bil Iman, wa la taj'al fi ƙulubina gillan lil-ladhina amanu, rabbana innaka Ra'ufur Rahim.

Ya Ubangijinmu! Ka gafarta mana da 'yan'uwanmu waɗanda

suka rigaye mu da Imani, kuma kada Ka sanya ƙiyayya a cikin zukatanmu ga waɗanda suka yi Imani. Ya Ubangijinmu, lalle Kai ne Mai tausayawa, Mai rahama.

- Allahumma, inni abduka, ibnu abdika, ibnu amatika, nasiyati biyadika, madin fiyya hukmuka, adlun fiyya qada'uka, as'aluka bikullis min huwa laka, sammaita bihi nafsaka, au anzaltahu fi kitabika, au ista'asarta bihi fi ilmil ghaibi indaka, an taj'alal Ƙur'anal azima rabi'a qalbi, wa nura sadri, wa jala'a huzni, wa zahaba hammi, Allahumma allimni minhu ma jahiltu, wa zakkirni minhu ma nussitu, warzuqni tilawatahu ana'al laili wannahari alal wajhil lazi yurdika anni, birahmatika ya arhamar rahimin.

Ya Allah! Lalle ni bawanKa ne, ɗan bawanKa, ɗan baiwarKa. Al'amari na yana hannunKa, hukuncinKa tabbatacce ne a kaina, hukuncinKa a kaina adalci ne. Ina roƙon Ka da duk wani suna da Ka sanya wa kanKa, ko Ka saukar a cikin LittafinKa, ko Ka ɓoye a cikin ilimin gaibinKa, Ka sanya Alƙur'ani mai girma ya kasance warakar zuciyata, kuma hasken ƙirjina, kuma maganin damuwata, da kawar da baƙin cikina. Ya Allah! Ka sanar da ni abin da ban sani ba a cikinsa, Ka tunatar da ni abin da na manta daga gare shi, Ka azurta ni da karanta shi cikin dare da rana, a yanayin da zai sa Ka yarda da ni. Da rahamarKa, ya Mafi jinƙan masu jinƙai.

- Allahumma, inni a'uzu biKa min azabi jahannama, wa min azabil ƙabri, wa a'uzu bika min fitnatil masihid dajjali, wa a'uzu bika min fitnatil mahya wal mamati, Allahumma, inni a'uzu bika minal ma'asami wal magrami.

Ya Allah! Ina neman tsarinKa daga azabar wutar jahannama, da azabar ƙabari, kuma ina neman tsarinKa daga fitinar Dujal, da fitinar rayuwa da mutuwa. Ya Allah! Ina neman tsarinKa daga zunubi da basussuka.

- Allahummag fir li, wahdini, warzuƙni, wa afini, warhamni, Alhumma, inni as'aluka khairal mas'alati, wa khairad du'a'i, wa khairan najahi, wa khairal amali, wa khai-rath sawabi, wa khairal hayati, wa khairal mamati, wa thabbitni, wa thaƙƙil mawazini, wa haƙƙiƙ Imani, warfa' darajati, wa-taqabbal salati, waghfir khaɗi'ati, wa as'alukad darajatil ula minal jannati, Amin.

Ya Allah! Ka gafarta min, Ka shiryar da ni, Ka azurta ni, Ka ba ni lafiya, Ka yi min rahama. Ya Allah! Ina roƙon Ka mafi alherin roƙo, da mafi alherin addu'a, da mafi alherin kuɓuta, da aiki mafi alheri, da lada mafi alheri, da alherin rayuwa, da Kyakkyawar mutuwa. Ka tabbatar da ni, Ka sanya mizanina ya yi nauyi, Ka tabbatar da Imanina, Ka ɗaukaka darajata, Ka karɓi Sallolina, ka gafarta min kurakurai na. Ina roƙon Ka maɗaukakiyar daraja a Aljanna, Amin.

- Allahumma, inni as'aluka fawatiḥal khairi, wa kha-watimahu, wa jawa-mi'ahu, wa awwalahu wa akhirahu, wa zahirahu wa baɗinahu, waddarajatil ula minal janna, Amin.

Ya Allah! Ina roƙon Ka alheri a farkon lamarina da ƙarshensa, da matattaran alheri, farkonsa da ƙarshensa, bayyane da ɓoyayyensa, da maɗaukakiyar daraja a Aljanna, Amin.

- Allahumma, inni as'aluka an tarfa'a zikri, wataḍa'a wizri,

wa tusliḥa amri, wa tuɗahhira ƙalbi, wa tuḥṣina farji, wa tunawwira ƙalbi, wa taghfira li zanbi, wa as'alukad darajatil ula minal jannati, Amin.

Ya Allah! Ina roƙon Ka Ka ɗaukaka darajata, Ka yafe zunubaina, Ka gyara al'amurana, Ka tsarkake zuciyata, Ka kare al'aurata, Ka haskaka zuciyata, Ka gafarta min zunubaina. Ina roƙon Ka maɗaukakiyar daraja a Aljanna, Amin.

- Allahumma, inni as'aluka an tubarika li fi nafsi, wa fi sam'i, wa fi basari, wa fi ruhi, wa fi khalƙi, wa fi khuluƙi, wa fi ahli, wa fi maḥyaya, wa fi mamati, wa fi amalī, wataƙabbal ḥasanati, wa as'alukad darajatil ula minal janna, Amin.

Ya Allah! Ina roƙon Ka Ka sanya min albarka, a jina da ganina, da ruhina, da halittata, a ɗabi'ata, da iyalina, da rayuwata, da mutuwata, da aikina. Ka karɓi kyawawan ayyukana. Ina roƙon Ka maɗaukakiyar daraja a Aljanna, Amin.

- Allahummah fazni bil Islami ƙa'iman, wah hfazni bil Islami ƙa'idan, wah fazni bil Islami raƙidan, wa la tushmit bi aduwwan wa la hasidan

Ya Allah! Ka bani kariya da Musulunci yayin da nake tsaye, da yayin da nake zaune, da yayin da nake kwance. Kada Ka sanya abokan gaba ko maƙiya da mahassada su yi min dariya.



- Allahumma, ba'id baini wa baina khaɗayaya kama ba'adta bainal mashriƙi wal maghrib, Allahumma, naƙƙini min khaɗayaya kama yunaƙƙas saubul abyadu minal danas, Allahummag silni min khaɗayaya bissalji wal ma'i wal baradi.

Ya Allah! Ka nisantar da ni daga zunubaina kamar yadda Ka nisantar da gabas da yamma. Ya Allah! Ka tsarkake ni daga zunubaina kamar yadda ake tsarkake farin tufafi daga datti. Ya Allah! Ka wanke ni daga zunubaina da ƙanƙara da ruwa da raɓa.

- Allahumma, anta'l Malik, la ilaha illa anta, anta Rabbi wa ana abduka, ẓalamtu nafsi, wa'atarraftu bizanbi, faghfir li dhunubi jami'an, in-nahu la yaghfiruz zunuba illa anta, wahdini li aḥsanil akhlaƙi, la yahdi li aḥsaniha illa anta, waṣrif anni sayyi'aha, la yaṣrifu anni sayyi'aha illa anta, labbaika wa sa'daika, walkhairu kulluhu biyadika, washsharru laisa ilai-ka, ana bika wa ilaika, tabarakta wata'alaita, astaghfiruka, wa atubu ilaika.

Ya Allah! Kai ne Mamallaki, babu abin bauta bisa cancanta sai Kai. Kai ne Ubangijina, ni kuwa bawanKa ne. Na zalunci kaina, kuma na yarda da zunubaina, don haka Ka gafarta mini dukan zunubaina. Lalle babu mai gafartawa sai Kai. Ka shiryar da ni zuwa kyawawan halaye, babu mai shiryarwa zuwa gare su sai Kai. Ka kawar da munanan halaye daga gare ni, babu mai kawar da su daga gare ni sai Kai. Na amsa kiranKa, Ka sanya farin ciki a raina, alheri gaba ɗaya yana hannunKa, kuma sharri ba ya zuwa gare Ka. Daga wurinKa nake neman dace kuma gare Ka nake neman mafaka. Ka ɗaukaka, kuma albarkatunKa sun yawaita. Ina neman gafararKa, kuma ina tuba gare Ka.

- Allahumma, inni a'uzu bika an uradda ila arzali'l 'umuri, wa a'uzu bika minal ƙaswati wal gaflati, waz zillati wal

maskanati, wa a'uzu bika minal kufri, wal fusūƙi, wash shiƙāƙi, wassum'ati, war riya'i.

Ya Allah! Ina neman tsarinKa daga jinkirtawa zuwa mafi munin tsufa. Ina neman tsarinKa daga kaushin zuciya da gafala da ƙasƙanci da talauci. Kuma ina neman tsarinKa daga kafirci da fajirci da taɓewa da jiyar da aiki da riya.

- Allahumma, inni a'uzu bi-ka min sharri ma amiltu, wa min sharri ma lam a'amal, wa a'uzu bika min sharri ma alimtu, wa min sharri ma lam a'lam.

Ya Allah! Ina neman tsarinKa daga sharrin abin da na aikata, da sharrin abin da ban aikata ba. Ina neman tsarinKa daga sharrin abin da na sani, da sharrin abin da ban sani ba.

- Allahumma, inni a'uzu bi-ka minal hadmi wat ta-raddi, wa minal garaƙi, wal haraqi, wal harami, wa a'uzu bika an yata-khabbaɗanish shaiɗanu 'inda'l mauti, wa a'uzu bi-ka an amuta ladigan, wa a'uzu bika min ɗama'in yahdi ila ɗab'in.

Ya Allah! Ina neman tsarinKa rugujewar abu a kaina, da faɗuwa, da nutsewa cikin ruwa, da ƙonewa, da tsufa. Kuma ina neman tsarinKa kada Shaidan ya ruɗe ni yayin mutuwa. Ina neman tsarinKa daga mutuwa ta hanyar cizon dabba mai cizo, kuma ina neman tsarinKa daga kwaɗayi da zai kai ga ɗabi'a mara kyau.



- Allahumma, inni as'alukas sabata fil amri, wal 'azima-ta 'alar rushdi, wa as'aluka shukra ni'imatika, wa husna 'iba-datika, wa as'aluka ƙalban saliman, wa lisanan ṣadiƙan, wa as'aluka min khairi ma ta'alamu, wa a'uzu bika min sharri

ma ta'lamu, wa astaghfiruka mimma ta'lamu, wa anta 'allamul guyub.

Ya Allah! Ina roƙon Ka dawwama a kan addini, da tabbatuwa a kan shiriya. Ina roƙon Ka Ka bani ikon gode wa ni'imarKa, da kyautata ibada gare Ka. Ina roƙon Ka zuciya mai tsabta, da harshe mai faɗin gaskiya. Ina roƙon Ka alherin abin da Ka sani, kuma ina neman tsarinKa daga sharrin abin da Ka sani. Ina neman gafararka daga abin da Ka sani, lalle Kai ne Masanin gaibu.

- Allahumma, alhimni rushdi, wa ƙini sharra nafsi, ya Ḥayyu ya Ƙayyumu, Allahumma, zidni wa la tanƙuṣni, wa akrimni wa la tuhinni, wa a'ɗini wa la taḥrimni, wa'asirni wa la tu'sir 'alayya, ya zal jalali wal ikram.

Ya Allah! Ka shiryar da ni, Ka tsare ni daga sharrin kaina, Ya Rayayye, Ya tsayayye da zatinSa. Ya Allah! Ka ƙara min falalarKa, kuma kada Ka rage ni, Ka karrama ni, kada Ka sa na wulaƙanta, Ka ba ni, kada Ka hana ni. Ka fifita ni, kada Ka fifita wani a kaina, Ya Mai girma da karamci.

- Allahumma, inni as'aluka raḥmatan min 'indika, tahdi biha qalbi, wa-tajma'u biha amri, watal-lummu biha sha'athi, wa-taḥfaẓu biha ga'ibi, wa-tarfa'u biha shahidi, wa-tubayyidu biha wajhi, wa-tuzakki biha 'amalī, wa-tulhimuni biha rushdi, wa-taruddu bihal fitana 'anni, wa ta'aṣimuni biha min kulli su'in.

Ya Allah! Ina roƙon Ka rahama daga gare Ka, wadda za Ka shiryar da zuciyata da ita, Ka kuma gyara al'amurana, Ka yafe

tuntuɓe na, Ka kiyaye abin da na bari a bayana, Ka ɗaukaka ni, Ka haskaka fuskata, Ka tsarkake aikina, Ka shiryar da ni, Ka kawar da fitintinu daga gare ni, Ka tsare ni daga kowane sharri.

- Allahumma, inni as'aluka ṣihhatan fi iman, wa imanan fi husni khuluƙin, wa najahan yatba'uhu falahun, wa raḥmatan minka, wa 'afiyatan minka, wa magfiratan wa riḍwana.

Ya Allah! Ina roƙon Ka ingantaccen Imani, da Imani cikin kyawawan halaye, da nasara wadda take biye da samun rabauta, da rahama daga gare Ka, da lafiya daga gare Ka, da gafara da yardarKa.

- Allahumma, innaka tas-ma'u kalami, wa tara makani, wa ta'alamu sirri wa 'alaniyyati, la yakhfa 'alaika shai'un min amri, wa anal bā'isul faƙīru, wal mustagīsul mustajīru, wal wajilul mushfiƙu, al-muƙirrul mu'uatarifu ilai-ka bizanbihi, as'aluka mas'alatal miskīni, wa ab-tahilu ilaika ibtihālal muz-nibiz zālīl, wa ad'ūka du'a'al khā'ifid darīr, du'a'a man khada'at laka raƙabatuhu, wa zalla laka jismuhu, wa ragima laka anfuhu, fa Allahumma, taƙabbal tawbatī, wagsil ḥaubatī, wa ajib da'awatī, wa sabbit hujjatī, wahdi ƙalbī, wasaddid lisānī, waslul sakhimata ṣadri, ya arḥamar rāḥimīn.

Ya Allah! Lalle Kai Kana jin maganata, Kana ganin inda nake, kuma Kana sane da baɗinina da zahirina. Ba wani abu daga al'amurana da yake ɓoye a gare Ka. Ni miskini ne matalauci, wanda yake neman taimako daga gare Ka, mai tsoron Ka, mai tabbatar da zunubansa, mai roƙon Ka irin roƙon miskini.

Ina roƙon Ka irin roƙon mai zunubi mai ƙasƙantar da kai. Ina roƙon Ka irin roƙon mai tsoron Ka, irin roƙon wanda ya risina gare Ka, ya kuma ƙaskantar da kansa gare Ka. Ya Allah! Ka karɓi tubana, Ka wanke zunubaina, Ka karɓi addu'ata, Ka tabbatar da hujjata, Ka shiryar da zuciyata, Ka daidaita harshena, Ka kawar da ƙiyayya daga cikin zuciyata, Ya Mafi tausayin masu tausayi.

- La ilaha illa anta sub-hanaka inni kuntu minaz zālimīn.

Babu abin bautawa bisa cancanta sai Kai. Tsarki ya tabbata gare Ka! Lalle ni na kasance cikin azzalumai.

- Rabbana 'alaika tawak-kalna, wa ilaika anabna, wa ilaikal maṣīr, Rabbana la taj'alna fitnatan lillazīna kafarū, wagfir lana rabbana, innaka antal azīzul ḥakīm.

Ya Ubangijinmu! Da Kai muka dogara, gare Ka muke tuba, kuma gare Ka makoma take. Ya Ubangijinmu! Kada Ka sanya mu fitina ga waɗanda suka kafirta, Ka gafarta mana, Ya Ubangijinmu! Lalle Kai ne Mabuwayi, Mai hikima.

- Subhana rabbika rabbil 'izzati 'amma yasifūn, wa salāmun 'alal mursālīn, walḥamdu lillahi rabbil 'ālamīn.

Tsarki ya tabbata ga Ubangijinka, Ubangijin buwaya daga abin da suke siffantawa. Aminci ya tabbata ga Manzanni, godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai.

Walḥamdu lillahi awwalan wa ākhiran, wa ṣallallahu wa Sallama 'ala nabiyyina Muḥammadin, wa alihi, wa ṣaḥbihi ajma'īn.

Dukkan godiya ta tabbata ga Allah a farko da ƙarshe. Allah Ya yi daɗin tsira da aminci ga Annabinmu Mu-hammadu da Alayensa da Sahabbansa bakiɗaya.

# Abubuwan da ke ciki

Gabatarwar Hukumar Masallatai Biyu Masu Alfarma ........ 4
Gabatarwa ........ 6
Miƙatai da ɗaukan harama ........ 8
Tambihi ........ 10
Rukunan Umara Da Wajibanta Da Sunnoninta ........ 11
Abubuwan Da Aka Haramta Wa Wanda Ya Ɗau Harama ........ 12
Kashe-Kashen Abubuwan Da Aka Haramta Ta Fuskar Fidiya (Fansa) ........ 14
Yadda Ake Umara ........ 16
Zaɓaɓɓun Addu'o'i ........ 20
Abubuwan da ke ciki ........ 43

حرمين

رئاسة الشؤون الدينية
بالمسجد الحرام والمسجد النبوي